# THE DISABILITY LAW

Popular Version

[Hausa]

# CONTENTS

Gabatarwa 1
Dokar Nakasa 3
Sashi Na 1 - Yacin Ga Rayuwan Iyali Da Hidimomin Rayuwa 4
Sashi Na 2 - Bambamcin Kulawa Dangane Da Wurin Zama 5
Sashi Na 3 - Sharudan Zama a Wurare Na Musamman Da Aka Kafa 5
Sashi Na 4 - Cin Amfani Da Nuna Wa Mutumin Da Ke Fama Da Nakasa Bambamci 6
Sashi Na 5 - Mai Nakasa Ya Zamanto Da Shi Ake Yin Komai Wajen Shari'a 6
Sashi Na 6 da 7 - Daman Samun Zuma Wurin Da Jama'A Ke Zuma Da Yin Aiki 7
Sashi Na 8 - Hukumci Ga Karya Doka 7
Sashi Na 9 - Kafa Cibiyoyin Daukan Aiki Ga Mutanin Dake Da Nakasa 7
Sashi Na 10 - Bunkasa Aiki Ga Masu Nakasa 8
Sashi Na 11 - Tanadin Kayan Aiki 8
Sashi Na 12 - Turawa, Dauka Da Sake Daukan Nakasasshe Aiki 8
Sashi Na 13 - Horo Mai Dacewa Ga nakasassun Da Basu Da Aiki 9
Sashi Na 14 da 15 - Cibiyoyin Tsugunarwa Da Wurin Tsugunar Da Al'Umma 10
Sashi Na 16 - Ilimantar Da Yaro Mai Nakasa 10
Sashi Na 17 - Kayan Karatu Da Na'Urori a Makarantu 11
Sashi Na 18- Bada Ilimi Akyauta Da Makarantu Na Musamman 11

Sashi Na 19 - Bada Horo Da Ya Dace Ga Wadanda Suka Gama JSS 11
Sashi Na 20 - Kin Daukar Mai Nakasa Ajiki Amakaranta Sabili Da Nakasa 12
Sashi Na 21 - Za'Abada Karatu Na Musamman Amakarantun Kere-Kere Da Na Koyon Sana'Ar Hannun Da Na Horar Da Malumma 12
Sashi Na 22 - Kayan Laburari 13
Sashi Na 23 - Darajan/Muhimamancin Bukatar Masu Nakasa Ajiki 13
Sashi Na 24 - Shigowa Da Abin Hawa Da Doka Bata San Da Shi Ba 13
Sashi Na 25 - Mai Nakasa Ajiki Mai Tafiyar Kasa 14
Sashi Na 26 - Wurin Ajiyan Abin Hawan Masu Nakasa Ajiki 14
Sashi Na 27 - Mallakan Lsisin Tuki 15
Sashi Na 28 - Kayan Amfani Masu Nakasa Ajiki a Tashoshin Jirage 15
Sashi Na 29 - Kebe Wurin Zama Amotoci 15
Sashi Na 30 - Hukunci Masu Saba Sassa Doka Na 26 to 29 16
Sashi Na 31 - Kula Da Lafiya 16
Sashi Na 32 - Horrar Da Ma'aikatan KiWon Lafiya 16
Sashi Na 33 and 34 - Shirye-Shiryen Kiwon Lafiya Da Binciken Lafiyar Yaran Makaranta Lokaci-Locaci 17
Sashi Na 35 - Kafa Cibiyoyin Hasashe 17

Tanade-Tanade Na Musamman

Sashi Na 36 18
Sashi Na 37 - Lakabin Banza 18

Sashi Na 38 - Daman Zuwa Harkokin Wasanni Ko Bukukuwa Ko Kuma Shagulgulan 18
Sashi Na 39 - Samun Daman Shiga Harkokin Kasa 19
Sashi Na 40 - Karfa Doka Da Masu Nakasa Ajiki 19
Kafa Majilisor Masu Ajiki Ta Kasa Da Ayyoken Malalisar 20
Sashi Na 60 - Dokar Wucin Gadi 20

# GABATARWA

Shigar da dokan 715 da majalisan jamhoriyyan Ghana ta hudu ta yi ya kawo babban nasaran mahawara ga wadanda ke fama da nakasa (PWDS). Anyi dokan ne don aga cewa amsu fama da nakasa na more 'yancin bayani ko article na 29 na kundin tsarin mulkin Ghana 1992, tare da tsinkaya ciyar da ingancin rayuwan nakasassu da kuma ainihin hidimomin nakasassu.

Dokan 715 ta lamunce ma nakasssu daman zuwa wurare mallakan gwamnati, karban magani a asibitin gwamnati da na musamman kyauta, ilimi, bada aiki da sufuri (transportation).Dokar ta 715 ta tsara wajibci da wasu hakkoki na ma'aikatun gwammanti da na 'yan kasuwa.

Dokan 715 zata tabbatar da kirkiro 'desk' na nakasassu a cibiyoyin aiki dabam- dabam a kasa baki daya, kuma dokan zata sake samara da kafa wata majalisa ko 'council' ta kasa akan mutannin da ke fama da nakasa ko nakasassu. Zaman da aka yi wa kafa dokar yayi tanadi na tsawon shekara 10 (MORATONIUM) ga kiyaye dokar tare da tanade- tnaden samu da iya shiga ko ina

saboda ba wadataccen jari da ake bukata ya kasance dukan gine-ginen  gwamnati dake da wahala ya zamanto sauki ga su nakassasu.

Kaman yawancin dokoki kasa, dokan 2006 (doka 715) tana da yawa ko fadi (VOLUMINOUS),kuma misalain  sun nuna cewa yawancin nasu karantawa su kan sha wahalan gaske wajen zurfafa bincike. Kari akan wannan, akwai misalai da yawa inda kopis (coppies) na dokokin gwamnati nutane suka kasa samu don karantawa.Idan aka yi la'akari da irin wahalan da kungiyoyin da abin ya shafa wajen kamun kafa ko bada shawara kafin dokan ta samu shiga ko karbuwa, akwai bukatan ba wadanna matsaloli muhimmanci ganin cewa sune suka haiffar da tarnakin aiwatar da dokokin da aka kafa a baya, wajibi ne ayi maganin haka a yanzu don a yi maganin cin karo. Dangane da haka cibiyar ta i hobbasa (initiative) ta samar da takaitaccen bayinin dokan don a raba ma jama'a (public dissemination), sabo da a kara taimaka ma fahimta, haka zlika a kara yi ma jama'a gangami don su san 'yancin masu fama da nakasa acikin Ghana.

Majalisar jamhoriyyan Ghana ta amince da kudirin nakassa ya zama doka a shekaran 2006. Makasudin wannan doka shine ya kare da kuma yin yaki ga 'yanci da karamci (respect) ga mutani da ke rayuwa tare da nakasa. A yawanci lokuta, ba a cika girmamasu kaman mu ba. Iyali da alumma so tari. sukan juya ma mutain dake da nakasa baya. Wadanda suke cin karo da wannan hali a kullun akan kaisu wurin kula da nakassasu da jama'a basu kulawa dasu sosai.Don haka,dokja zai tabbatar cewa lalle masu nakasa sun more ma 'yancin su, wanda ke kushe a cikin kundin tasrin mulkin mu.

Har idan mutum ya kasance nakassashe ne (shine "mutum nada nakasa") kenan ya nuna cewa mai fama da nakassan na da matsala a wani bangare na jiki ko hankali.

Tunda dan taliki nada matsala a wani bangare na jiki, mutum ba zai iya yin tafiya, baya iya yin amfani da ido da sauran su. Wasu lokuta mai fama da nakassa baya iya yin komai saboda

wadannan matsaloli samu cudanya acikin jama'an shi yana yin wuya.

## SASHI NA 1

### YANCIN GA RAYUWAN IYALI DA HIDIMOMIN RAYUWA

So tari, mutanen da suke nakassassu basu jin dadin zama da 'yan uwansu na dangi. Akan kyale su subar gidajensu ba gatanci. Wasu lokuta ba a yadda su yi wasa da wasu mutane da aki yi imanin cewa suna iya kamuwa da cuta ko nakassan da suke da shi.

Muna kuma ganin cewa nakassasu basu iya yin wani tunani, kirkiro abubuwa ko yin wani abu na kansu. Wadannan tunani akan hanyan da basu dace ba da bada labarai na karya, wanda mutane akullun sukan fadi game da nakassasu.

Kuskure ne kuma ya saba ma doka a hana masu fama da nakasa daga more rayuwa a cikin dangi ko shiga cikin wani bangare na rayuwa, kirkiro wani abu ko shiga cikin jama'a don wani hidima ko nishadi.

## SASHI NA 2

### BAMBAMCIN KULAWA DANGANE DA WURIN ZAMA

Idan mutu mai nakasa yana yin haya a gida mai gida, ko mai lura da gidan bai dece ya kyamaci mai nakassa ba.Wajibi ne mai gida ya kula da mai fama da nakasa kamar yadda ya lura da mara nakasa.Doka bata yarda da wannan bambamci ba. Haka idan nakasasshe na son taimako don ya ji dadin rayuwa wjibin mai gidan ne ya yi hakan.

## SASHI NA 3

### SHARUDAN ZAMA A WURARE NA MUSAMMAN DA AKA KAFA

Idan ya zama wajibi ga mutumin da ya kamu da nakasa zai gina "gida" na musamman, makaranta (school) ko wata cibiyan karatu, abinda ke akwai ko sharuda zai kassance daidai da mutumin da ba shi da nakasa kuma shekarunsu guda.To amma,har idan mai nakasa nada wasu bukatu na musamman,yana iya zamantowa akawo sharuda da za su bambamta don gamsar da bukatu na musamman.

## SASHI NA 4

### CIN AMFANI DA NUNA WA MUTUMIN DA KE FAMA DA NAKASA BAMBAMCI

Doka ta yi tir da ayi amfani da mutumin da ke fama da nakasa ta hanyan da ba ta dace ba don biyan bukatan kanka. Alal misli, ba daidai bane ayi amfani da yaro mai nakassa wajan naiman kudi a maimakon kai yaro makaranta (school) ya koyi wata dabara ko aiki. Kada akula da nakasasshe da mummunan niyya sabo da nakassa.Wajibine idan nakasasshe na iya yin aiki da kowa ke iya yi abiyashi hakkinshi kamar yadda ake biyan kowa. Ya dace a girmama nakasasshe kada aci masa mutumci sabo da nakasan shi.

## SASHI NA 5

### MAI NAKASA YA ZAMANTO DA SHI AKE YIN KOMAI WAJEN SHARI'A

Idan mutum mai nakassa ya je kotu, kotun ya kamata ya taimaka har shi nakasasshen ya gamsu da ma murnan yadda aka ci shari'a. Alal misali idan mai nakasan kurma ne,kotu sai ta nemo wanda ya san maganan kurmaye yayi masa bayanin abin da kotu ke ciki.

## SASHI NA 6 DA 7

### DAMAN SAMUN ZUWA WURIN DA JAMA'A KE ZUWA DA YIN AIKI

Wadanda ke yin kasuwanci ko suke yi ma jama'a aiki a wuraren da sai an hau sama ko bisa irin su shago, wurin sayar da abinci, ko asibiti, wajibi ne abi abinda doka ta ce. Doka tace a tabbatar an tanadi yadda nakasasshe zai iya hawa wurin cikin sauki.

## SASHI NA 8

### HUKUMCI GA KARYA DOKA

Duk wadan yaki bin dokokin ko wasu daga ciki kuma ya karya wasu ana zuwa da shi kotu, kuma in aka samu mutum da laifi, ma'anan mutum da gaskel bai kula da nakasshe yadda ya dace ba, kotu na iya daure mai laifi na tsawon wata uku (3) ko biyan kudi ko duka.

## SASHI NA 9

### KAFA CIBIYOYIN DAUKAN AIKI GA MUTANIN DAKE DA NAKASA

Daya daga cikin dalilain yin doka shine a taimaka ma wandanda keda nakssa su samu

ayyuka don su daina baran abinci da kudi a tituna (streets) don haka, gwamnati ta tanadi cibiyoyi ko wuraren da za'a taimaka ma masu fama da nakassa su samu aikin yi.

## SASHI NA 10

### BUNKASA AIKI GA MASU NAKASA

Ba lallai gwamnati kadai bace, zata sama ma nakasassu ayyukan yi ba wadanda ke sana'ar kansu na iya taimakawa.Gwamnati zata karfafa ma wadanda ke aikin kansu ko kanfanoni (companies) gwiwa ta hanayan kyale su su ki biyan wasu haraji (taxes).

## SASHI NA 11

### TANADIN KAYAN AIKI

Idan gwamnati ko kamfani, mai zaman kanshi ya dauki mutum mai nakasa aiki, wadanda suka dauke shi aikin zasu bashi kaya da abubbuwan da yake naima do yayi aikin da kyau.

## SASHI NA 12

### TURAWA, DAUKA DA SAKE DAUKAN NAKASASSHE AIKI

Wadanda da keda nakassa za su bukaci yananyi na musamman don su yi aiki. A don

haka, idan wadannan nakasassun an dauke su aiki kuma ya kasance suna jin dadin inda suke aikin,wanda ya daukesu aikin bai dace ya sake musu wurin aiki da zai kawo musu damuwa.Idan matsalan da mai nakasa ya samu ya faru ne hadarin wurin aiki,ba daidai bane wanda ya dasukeshi aikin ya kore shi.Doka ta yarda wanda ya dauke shi aiki ya horar da nakasasshen sabon aiki kuma ya tura shi inda zai iya yin aiki.Wurin sabon aikin kuma ya kasance akwai sharudan da za su dace da naksan da a samu mutum. Za ayi wadannan duka hadi da biyan shi kudi saboda nakassan daya samu yayin da yake yi ma mai aiki hidima (aiki)

## SASHI NA 13

### HORO MAI DACEWA GA NAKASASSUN DA BASU DA AIKI

A matsayin wani bangare na shirin taimaka ma nakasassu su samu ayyukan yi, doka tace gwamnati za ta rubuta sunaye da kuma jeranta mutanin da keda nakasa wadanda ba su da aiki don a taimaka su samu aiki.In bayan shekara biyu, masu nakasa basu samu aiki ba,gwamnati zata taimaka ta horar dasu su samu dabarun da

suka wajaba da kuma basu kayan aiki, haka zalika a basu rance kudi don su fara sana'a. Amma doka ta hana mai fama da nakasa ya kwashe kayan da ak bashi don ya ingata rayuwanshi ya sayar.In aka kama mutumin da ya yi hakan, doka zata hukumta shi ta hanyan dauri na shekara guda.

## SASHI NA 14 DA 15

### CIBIYOYIN TSUGUNARWA DA WURIN TSUGUNAR DA AL'UMMA

Yawancin lokuta mutanin da ke fama da nakasa na bukatan taimako da kulawa da shawara don su iya yanke muhimin shawara akan wani abu, misali, aikin da za suyi don su ji sun yarda suna aikin bangaren al'umma. Doka taba gwamnati aikin kafa cibiyoyi inda za a kula da nakasassu don su dinga mantawa da hali da suke ciki.Ana iya kiran wannan tsugunarwan tsugunar da nakasassu da zai dada karfafa musu gwiwan cudanya cikin al'ummansu.

## SASHI NA 16

### ILIMANTAR DA YARO MAI NAKASA

Dukan iyaye, marika ko kulawa ko wanda ke lura da yaro mai nakassa wanda shekarun shi ya

kai zuwa makaranta (school) ayi kokari a kai yaron makanta. Makantan tana iya zama wadda kowa ke zuwa ko makaranta ta musamman in har shi yaron (NAKASASSHE) ya bukaci yin hakan.

## SASHI NA 17

### KAYAN KARATU DA NA'URORI A MAKARANTU

Za'aba makarantun kowace jiha kayan karatu da zai ba yaran makaranta masu nakasa ajiki daman cin amfanin makarantun.

## SASHI NA 18

### BADA ILIMI AKYAUTA DA MAKARANTU NA MUSAMMAN

Kananan yara masu nakasa ajiki zasu samu ilimi akyauta. Za'agina makarantu na musamman ga masu nakasa ajiki wadannda basu iya zuwa makaraantu na jama'a dangani da nakasa dake tare dasu.

## SASHI NA 19

### BADA HORO DA YA DACE GA WADANDA SUKA GAMA JSS

Alhakin gwamanti ne a bada horo na tsawon shekaru biyu ga wanda ya gama karatun JSS da

bai samu abin yi ba kuma bada wata-wata ba bayan gama karantun nasa. Haka Zalika gwamnati zata horar da mai nakasa ajiki da ya gama karatun JSS da ba zai iya ci gaba da karantun nun sa har zuwa wani matsayi ba.

## SASHI NA 20

### KIN DAUKAR MAI NAKASA AJIKI AMAKARANTA SABILI DA NAKASA

Idan iyaye ko mai kula da yaro suka yi niyyar kai yaransu masu nakasa ajiki a makarantun jama'a, doka bata ba wani jami'i (ie babban malami ko shugaban makaranta ko kuma mai kula da makarantan) yaki daukar yaro sabili da nakasa sai dai yaron na fama da nakasa day a zama wajibi yaje makaranta ta musamman.Duk wani malamin makaranta da yaki daukar yaro saboda nakasa ana iya daureshi na tsawon wata uku (3)

## SASHI NA 21

### ZA'ABAdA KARATU NA MUSAMMAN AMAKARANTUN KERE-KERE DA NA KOYON SANA'AR HANNUN DA NA HORAR DA MALUMMA

Ministan ilimi zai kula da ganin cewa an kafa wani horo na musaman amakaranta da wuraren

sana'a domin ilmantar da yara masu nakasa ajiki su koyi manager kurmaye da amfani da abin karatun makafi

## SASHI NA 22

### KAYAN LABURARI

Za' asa kaya da zasu taimaka wa masu nakasa ajikinsu su yi nazari a laburarin jama'a akan duk bukatunsu

## SASHI NA 23

### DARAJAN/ MUHIMAMANCIN BUKATAR MASU NAKASA AJIKI

Idan wata hukuma na neman tsara sha'nin sufurinta (that is hanyoyi da gadoid da wurin ajiyan abin hawa) hukumar zata tuna masu nakasa ajiki wurin yin tsarinta ko gininta ko kuma abin hawanta

## SASHI NA 24

### SHIGOWA DA ABIN HAWA DA DOKA BATA SAN DA SHI BA

Doka tana so ta bada dama kuma ta saukaka wa sasu nakasa ajiki suyi bulagoro zuwa ko ina. Don haka taba duk wani mai nakasa ajiki daman

shigowa da abin hawa acikin kasar ko wani abin da zai saukaka kai kawon masu nakasa ko kuma wani abin da zai dace da irin nakasar tasu. Idan wannan abin hawa ya shigo kasar ba za'akarbi haraji ba kamar yanda sauran jama'a ke biyan haraji idan sun shigo da abin hawa. Amma yakamata mu gane cewa rashin biyan harji ba zai bamu dama aika wa'yannan abin hawa zuwa wata kasa ba.

## SASHI NA 25

### MAI NAKASA AJIKI MAI TAFIYAR KASA

Motoci zasu dakata suba mai nakasa ajiki dake tafiyar kasa daman ketare titi idan yana da niyyar yin hakan. Hakan zai iya faruwa idan masu tafiyar kasa ke ketare titi, ko ako ina, musamman ma inda akayi wa masu nakasa ajiki da su ketare tiiti.

## SASHI NA 26

### WURIN AJIYAN ABIN HAWAN MASU NAKASA AJIKI

Yakamata duk wurin ajiyan motoci na gwamnati ko na masu zaman kansu akebe inda masu nakasa ajiki zasu ajiye nasu abin hawa kuma wannan wurin ne yakamata afara kebewa.

## SASHI NA 27

### MALLAKAN LSISIN TUKI

Yana iya kasancewa mutum nada nakasa na kurmanci,duk da haka zai iya cancanta abashi lasisin in har ya ci jarrabawan tuki kuma ya gamtsar da sharudan da hukumar kula da lasisin motoci da direbobi suka ajiye.

## SASHI NA 28

### KAYAN AMFANI MASU NAKASA AJIKI A TASHOSHIN JIRAGE

Za'asamar da kayan afanin masu nakasa ajiki afilin jirgin sama da jirgin ruwa da zasu saukaka wa masu nakasan su amfana da baki dayan tshoshin sukar jiragen.

## SASHI NA 29

### KEBE WURIN ZAMA AMOTOCI

Sabili da masu nakasa ajiki basu iya rigimar shiga mota da masu lafiya, doka ta bukaci akebe wurin na musamman amotocin haya da bos-bos domin masu nakasa ajikin su wala.

## SASHI NA 30

### HUKUNCI MASU SABA SASSA DOKA NA 26 TO 29

Idan wani yaki biye wa sassan dokar na 26 da 30 babu shakka ya saba ma baki dayan kokar, kumar doka zata ci shi tara ko kuma ta daureshi har tsawon wata uku (3) ko kuma ta dora masa hukuncin biyun duka.

## SASHI NA 31

### KULA DA LAFIYA

Hakkin mai tsananin nakasa ajiki ne kwararren likita ya kula da lafiyarsa akyauta. Haka zalika ba zasu biya wai bashin jinya ba ko wata na'ura da aka musu amfani da su.

## SASHI NA 32

### HORAR DA MA'AIKATAN KiWON LAFIYA

Sabili da ataimaka wa liktoci da sauran ma'aikatan kiwon lafiya kamar nesi-nesi kuma kara sanin bukatar kiwon lafiyar masu nakassa ajiki da sanin matsaloli da irin hali da suke ciki don su kula da su da kyau, dokar tace wa'yannan ma'aikatan kiwon lafiyar zasu koyi wasu karatu

akan masu nakasa da wasu abubuwa da suka shafesu alokacin da ake basu horon

## SASHI NA 33 - 34

### SHIRYE-SHIRYEN KIWON LAFIYA DA BINCIKEN LAFIYAR YARAN MAKARANTA LOKACI-LOKACI

Haka kuma kukumar ilimi zata kara karatun nakasa da wasu abubuwa da suka shafi naksan acikin tsarin shiriye-shiriyen kiwon lafiyar makarantun primary.

Bugu da kari hukumar kiwon lafiya kuma zata hada guiwa da hukumar ilimin sumai da handali su rika kula da lafiyar yaran makarantar akai-akai.

## SASHI NA 35

### KAFA CIBIYOYIN HASASHE

Ma'aikatar kiwon lafiya zata yi aiki tare da majalisun kananan hukumomi da kuma Ma'aikatar jin dadin rayuwa (SOCIAL WELFARE)don asamar da cibiyoyi ga iyaye mata da yara kanana don arika basu kulawa daga lokaci zuwa lokaci acikin gundumomi don ayi saurin gane cewa ko sun kamu da wata nakasa.

## SAHSI NA 36

Idan wani ya kera mashini acikin kasar (kamar mashinin wanki) wanda zai amfani nakasassu,ba za'akarbi wannan mutum haraji akan abin day a keran ba.

## SASHI NA 37

### LAKABIN BANZA

Doka tace ba daidai bane wani ya zagi nakasasshe da nakasar jikinsa.Duk wanda doka zata kamashi da wannan laifi zata daureshi har tsawon wata uku (3).

## SASHI NA 38

### DAMAN ZUWA HARKOKIN WASANNI KO BUKUKUWA KO KUMA SHAGULGULAN

Hukumar ilimi da wasanni zata guima da kananan hukumomi da komishan gargajiya su tabbatar da ganin cewa masu nakasa ajiki sun samusauki zuwa wuraren wasanni da gargajiya

kuma su samu daman sa kansu acikin wasannin da gargajiya.(5)

## SASHI NA 39

### SAMUN DAMAN SHIGA HARKOKIN KASA

In ya dece wani abu na faruwa acikin kasa ko jiha ko gunduma yakamata masu shirya wanan buki su tsara shi ta yanda masu nakasa ajiki zasu samu daman sa ki.

## SASHI NA 40

### KARFAFA DOKA DA MASU NAKASA AJIKI

In yan doka (kamar iyan sanda etc) suka kama ko suka tsore mai nakasa ajiki, yakamata su kula da irin nakasa dake tare dashi kuma su bashi taimekon da zai bukaci. Bugu da kari doka ta bukaci su iyan dokan su samu horo aken zance nakasa.

## KAFA MAJILISOR MASU NAKASA AJIKI TA KASA DA AYYOKEN MALALISAR

Dafa majalisor masu nakasa ajiki ta kasa ka ayyoken malalisar

Dokar tace an kafa majalisar masu nakasa ajiki ta kasa. Wannan majalisa zata bada shawara akan gudunmuwa da yakamata aba masu nakasa ajiki da kuma shawara akan shirya dbaru da zai had da masu nakasa ajiki wurin shirya harkokin ci gaban kasar

## SASHI NA 60

### DOKAR WUCIN GADI

Sabili da tsadar sake ginin da masu nakasa ajiki basu iya yin amfani dashi, dokar ta shwarci masu irin wa'iyannen gidaje da su sake ginin nasu tsakanin shekaru goma. Masu gidagen da suka yi gininsu kafin bullowan wannan doka su sake ginin nasu ta yanda masu nakasa ajiki zasu iya yin amfani da ginin acikin sauki.